# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Yesu ya zabi Masu Taimako guda Goma sha biyu




**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**



**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**




**Yesu ya yi abubuwa masu ban mamaki. Ya warkar da cututtuka, ya ba da salama ga mutanen da suke cikin damuwa a zukatansu da tunaninsu, ya koyar da Kalmar Allah.**




Rundunan mutane suka zo wurin Yesu don neman taimako da warkarwa.  Sai ya zabi maza goma sha biyu daga masu binsa, domin su taimake shi a cikin aikinsa na Allah.
3


Idan akwai abubuwa na musamman da kake so ka yi zabi daga ciki, ka kan yi addu'a ga Allah?  Yesu ya yi!  A tuddun marar surutu a wurin da babu kowa, ya yi magana da Ubansa wanda ke cikin Samaniya.  Yesu ya yi addu'a har faduwar rana.
4


Yesu ya yi addu'a duka tsawon dare mai duhu.
5


Da sassafe, Yesu ya kira mabiyansa – duka abokan da sun yi masa hidima sun kuma yi masa biyayya.  Daga cikinsu ya zabi guda goma sha biyu domin su zama mataimaka na musamman, ko kuma ma'aika.
6


Guda biyun da Yesu ya fara zaba 'yan'uwa ne su, Siman Bitrus da Andirawus.  Suka bar kasuwancinsu na kama kifi sa'ad da Yesu ya fara kiransu domin su bi shi.
7


Yakubu da Yohanna, 'ya'yan Zebidi, su ma sun bar ragar kama kifin su.
8

Ya kuma zabi Filibus, Batilomi, Matiyu, Toma, Siman mai kwazo, Yakubu dan Halfiyos, Yahuda dan’uwan Yakubu, da Yahuda Iskariyoti wanda daga baya ya zama makiyin Yesu.



9

Yesu ya koyar cewa yin biyayya da Kalmarsa yana nan kamar gina gida a kan tushi mai karfi ne.  Iskar hadari mai tsanani ba zai taba rushe gidan ba.



10

Rashin biyayya ga kalmar Yesu ya zama kamar gina gida a kan yashi ne.  Sa’ad da iskar hadari ya taso, gidan zai rushe.



11

Wadansu umarnan Yesu ba su da sauki.  “Idan wani ya mare ka a kumatu na dama, ka mika masa na hagun kuma,” haka Ya koyar.  “Ka kaunaci abokan gabanka.”  Mutane suna bukatan taimakon Allah domin su iya yin rayuwa irin na Yesu.



12

Yesu ya kuma gaya wa mutanen su yi addu’a a boye – ba wai su yi addu’a a gaban mutane domin a gani ba kamar yadda wadansu shugabanin addini suke yi ba.



13

Yesu ya ce Allah zai ciyar ya kuma ba da sutura ga mutanen da suka amince da shi.  Tun da Allah yana ba da abinci ga tsuntsaye, yana ba da kala-kala masu kyau ga fure da filawa, Mutanensa za su iya amince da shi domin biyan dukkan bukatunsu.



14

Yesu ya koya wa sabobin masu taimakonsa abubuwa da dama a ranar. Bayan da ya gama, wani mai kuturta ya zo gareshi, yana rokon Yesu ya warkar da shi.



15

Yesu ya amsa wa kuturun, “Zan yi. Ka kasance da tsabta.” Sa’ada masu taimakon suke kallo, kuturtan ya bar shi. Sai ya warke! Dan Allah ne kadai zai iya yin haka. Masu taimakon sun sani cewa suna da Maigida mai kirki.



16

Yesu ya zabi Masu Taimako guda Goma sha biyu

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Matiyu 4-7, Markus 1, Luka 6

“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130

17

# KARSHE

39 60

18

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16

19